NEPU DA 'NEHUNCI' CIKIN SHEKARU 70: INA AKA KWANA DA GWAGWARMAYA?

Daga

Sunusi Umar Sadiq

Wasu matasa takwas, suka hadu su takwas, a ranar Takwas ga watan Takwas na shekara ta Dubu Daya da Dari Tara da Hamsin (8/8/1950) suka kafa jam'iyya mai manufofi takwas ba guda daya. A wani kaulin ma an ce sun yi zaman kafa wannan jam'iyya ne a gida mai lamba takwas, a Warri Street dake cikin Sabon Garin Kano. A makon da ya gabata wannan jam'iyya da matasan nan suka sanya mata suna NEPU tare da makala ma ta taken SAWABA, ta cika shekaru saba'in cif da kafuwa.

Shekaru saba'in lokaci ne mai tsawo. A tsakankanin wadannan shekaru abubuwa da yawa sun faru a kasar nan. A cikin wadannan shekaru saba'in, kasar ta samu 'yanci daga Turawan mulkin mallaka na Kasar Ingila. A cikin wadannan shekaru saba'in an sauya fasalin kasar a inda aka kirkiri jahar Midwest a shekarar 1963; daga baya ma aka bar tsarin lardi-lardi (regions) aka koma tsarin jaha-jaha (states), farko a shekara ta 1967, inda aka samar da jahohi goma sha biyu (12). Sai kuma 1975 inda jahohin su ka koma goma sha tara (19). Sai a 1987 inda aka kirkiri karin jahohi guda biyu suka zama jimillar su ashirin da daya (21). A shekarar 1991 aka samar da karin wasu jahohin goma su ka zama talatin (30). Sai kuma a shekarar 1996 inda suka zama talatin da shida (36).

Har wa yau a dai cikin wadannan shekaru saba'in an samu sauye-sauye ta fuskar tsarin mulki da ma salon gudanar da mulkin. Sojoji sun fatattaki farar hula. An yi yakin cikin gida, wato yakin basasa, na tsawon watanni talatin (30), shekaru biyu da rabi kenan. Bayan akalar mulkin kasar ta yi ta kara-kaina a tsakanin sojoji ta hanyar juye-juyen mulki, an kara dawowa turbar mulkin farar hula tare da sauya tsarin mulkin kasar daga wanda aka gada daga Ingila na Prime Minister (Parliamenatry/Westminster System) zuwa salon mulki na kasar Amurka mai tsarin shugaba mai cikakken iko (Presidential System).

Kari kan wadannan duka kuma shine rushe siyasar bangaranci da kabilanci ta yadda a yanzu doka ba ta amince da kafa jam'iyyu da suka takaita ga wani sashe na kasar nan ba ko kuma jam'iyyar ta zama ta iya 'yan wata kabilar ba ne. Domin a wancan lokacin akwai jam'iyyu irin su Borno Youth Movement (BYM) ta mutanen Borno; Ilorin Talaka Parapo (ITP) ta Yarabawan Ilorin;

United Middle Belt Congress (UMBC) wacce kusan ace ta 'yan kabilar Tiv ce kawai karkashin shugaban siyasar su na lokacin Mista J. S. Tarka. Haka dai misalan jam'iyyun wancan lokutan suke domin ko ita NEPU ai cikakken sunanta shine Northern Elements Progressive Union kuma aiyukanta kacokan da gwagwarmayar da ta yi a iya Arewacin Nijeriya ne.

Kusan duk lokacin da tattaunawa ta biyo kan gwagwarmayar NEPU ana ba da labari ne kan irin tsangwama da azaba da 'yan jam'iyyar da ma su goyon bayanta suka fuskanta karkashin ma su mulkin wannan lokacin. Ba kasafai ne za ka ji tattaunawa kan gundarin gwagwarmayar tafiyar ba, ma'ana manufofin da ita jam'iyyar NEPU ta sanya a gaba. Da za a yi irin wannan tattaunawar da watakila hakan zai zamar mana manuniya kan fahimtar hakikanin gwagwarmayar NEPU. Wace nasara aka samu? Ya akai aka samu wannan nasarar? A ina aka gaza? Me ya sa aka samu wannan gazawar? A wane hali ake ciki yanzu?

A takaicen takaicewa manufa da muradin NEPU su ne fada da tsarin kama-karya na hadakar sarakunan gargajiya da Turawan mulkin mallaka wanda ake kira Indirect Rule, wato tsarin da su Turawa ke tasarrufi da rayuwar jama'a amma ta hanyar amfani da sarakuna wadanda sune suke gudanar da komai. Dan haka a zahiri sarki ke mulki amma shi din ba komai ba ne face dodo-rido tunda tsare-tsare da dukkan umarni suna hannun Turawan. Aiwatarwa ce kawai aka damkawa ma su sarautar.

Lokaci ba abinda ya bari. A yau babu Turawan mulkin mallaka; sun bar mana kasar tun shekaru sittin da suka wuce. Sarakunan gargajiya kuma a yau sun zama hoto; ba sa nada alkalai ba sa shari'a. Haka kuma ba su da 'yan doka da kuma gidajen yari a karkashin ikonsu. Duk wadannan sauye-sauye sun faru a karkashin mulkin soja musamman ma a shekarun 1967 da kuma 1976.

Sai dai kuma duba na tsanaki zai nuna mana cewa bakon da ake murnar ya tafi ba fa tafiya ya yi ba. Salon yadda abubuwan suke tafiya ne kurum ya sauya. Zalunci da kama karya suna nan zagaye da mu cikin rayuwar mu ta yau da kullum. Babban tashin hankalin ma shine sabanin yadda a baya ba daidai ba take a matsayinta na ba daidai ba, a halin yanzu mun yi nisan da har ma ba daidan ba ita ake yiwa kallon daidai. Sabanin yadda a baya ake samun ma su yin fito na fito da abubuwan barna, a yau galiban mutane neman yadda su ma za su shiga cikin da'irar yin wannan barnar suke yi domin su ma a rika damawa da su.

Lokaci ya nuna wasu abubuwan da NEPU take kallon za su zama ma su amfani ga al'umma sun rikide sun zama barna. Tsarin kananan hukumomi na

daya daga cikin wadannan abubuwa. An samar da kananan hukumomi dan su zamanto ma fi kusanci ga jama'a. To amma a yau babu komai ciki sai almundahana, wawason dukiyar jama'a da babakere. Hatta lamarin zaben shugabannin kananan hukumomin ya zama wasan yara. Wannan abu ne da kowa ya sani ba sai an fada ba.

Wani karin misalin shine tabbatar da damar yin zabe ga kowa da kowa. Jam'iyyar NEPU ta yi adawa matukar adawa da tsarin zaben hawa-hawa saboda son ran da ake aiwatarwa karkashinsa. A karshe dai an dawo zaben falle daya a shekarar 1959. Mata kuma sun fara jefa kuri'a a shekarar 1979. Sai dai kuma wannan tsarin cike yake da damuwa. A wannan tsari da kare da rago duk darajar su daya. Maimakon sanin ciwon kai ya zama shine abun dubawa wajen kyale mutum ya zabi wadanda za su tafiyar da al'amuran kasa, sai kawai aka ce shekarun haihuwa kadai sune abun dubawa. A karkashin wannan tsari da hamshakin dan kasuwa mai masana'antu da kuma gafalallen matashi mai yawo kwararo-kwararo yana shaye-shaye da addabar jama'a duk matsayin kuri'arsu daya. Saboda haka wadannan gafalallun matasa sune da kunzumin kuri'unsu za su zabo baragurbin da zai zo ya dagula sha'anin tattalin arzikin kasa ta yadda wancan mai masana'antu zai durkushe! Ya Ilahiy ina hikima cikin wannan?

Jagora kuma shugaban jam'iyyar NEPU, Mallam Aminu Kano, ya na cewa babbar nasararsa a duniya ita ce koyawa talaka cewa 'na ki', 'ban yarda ba', 'ba haka za ai ba'. Sai dai bisa ga dukkan alamu Talaka ya manta da wannan karatun tuntuni. Yanzu kirarin da ake yiwa kusan kowane dan siyasa shine 'kowa ya bi'. Kuma wannan shine gaskiyar lamarin. A yau in ka ga ba abi dan siyasa ba to bai saki tsaba bane. Domin kuwa kaza a kullum mai zuba tsaba take bi. Ya ishe ka misali cewa lokacin da shi Mallam Aminu ya fito takarar zuwa majalisar taraiya ai abinda ake cewa shine:

Birni da kauye,
Mu zabi Aminu dan Talakawa.

Amma yanzu abinda za ka ji ana cewa shine: **'dan Sarki jikan Sarki!** ko kuma wani abu makamancin haka.

Saboda haka duk abubuwan da NEPU ta yi gwagwarmaya kan su suna nan tare da mu har zuwa wannan lokaci. Illa iyaka sun sauya kama. Duk da cewa yanzu Turawan mulki sun tafi to amma fa har zuwa wannan lokaci tattalin arzikinmu a hannun su yake. Duk da cewa an karbe duk wani iko daga sarakunan gargajiya to amma fa har yanzu akwai kashin dankali, danniya da kama karya. A zancen gaskiya ma abubuwan kara munana suka yi. A yau ana

kamawa a daure haka kurum. Shari'a ta zama tamkar ciniki. Mafitarka kawai shine me ka ke da shi me kuma za ka bayar. Ana kashewa ana daukewa har ma a batar da mutum ba tare da an yi wani abu akai ba. Rayuwar mutane na cikin hadari. Babu tsaron rayuka, dukiya da ma mutunci. Maganin abu a kasar nan shine kawai kar ka bari a yi maka, domin matukar an yin to fa ruwa ta sha.

Kamar yadda na fada har yanzu muna fama da kashin dankali. A halin da ake ciki yanzu a kasar nan abin lura kawai shine wa ka sani wa ya san ka, ko kuma wa ka sani wanda ya san wani. Sai ka ba da kudi za ka samu aikin yi. Sai ka ba da kudi za ka samu karin girma a wurin aiki. Kai ko da barin aikin ka yi to fa sai ka biya wani abu sannan hakkokinka na ma'aikaci za su fito. Haka abin yake hatta a fannin shugabanci da siyasa: sai ka ba da kudi za ka samu takara; sai ka ba da kudi za a zabe ka. Haka ma in wani mukami ne za ai maka a cikin gwamnati to fa shima sai ka biya! A irin wannan yanayin ya zaka yi tsammanin ma'akacin gwamnati ya zamo mai kwazo da jajircewa kan aikinsa? A irin wannan yanayi ya za ka tsammaci dan siyasa ya damu kansa da damuwar al'umma?

Saboda haka gwagwarmayar NEPU ba ta cimma gaci ba. Har yau ba a je inda akai kudurin zuwa ba. Wannan kuma ba boyayyen abu bane ga duk wanda ya san hakikanin tarihin tafiyar domin tun a wancan lokacin baraka ta samu ta yadda dukanin matasan nan guda takwas da suka kafa ta sai da suka fita daga cikinta. Wasu suka koma abokiyar hamaiyarta wato NPC. Wasu suka koma aikin gwamnati yayinda wasu kuma suka koma gefe suna gudanar da sha'anin rayuwarsu ta wasu fannonin daban-daban.

Maimakon taruwa kowace shekara, taro bayan taro, ana bayar da labarun su Tsalha Dankasa, Malami Koki, Sahabi Sokoto, Illa Ringim, Inuwa Buraji da sauransu, abinda ni nake ganin ya fi kyautuwa shine mu yi sabon kokarin tantacewa, tsefewa tare da tsara yadda gwagwarmayar NEPU ko kuma 'Nehunci' zai kasance a Nijeriyarmu ta yau. Gwagwarmayar a yanzu ba ta fito na fito da sarakuna ba ce. Su ma ta kansu suke yi yau! Ba kuma da Turawan mulkin mallaka ba ne. Alal hakika gwagwarmayar da ake bukata a Nijeriyar yau shine sauya tunanin Talakawa ta hanyar fito da su daga dimuwar da 'yan siyasar mu suka jefa su ciki ta yadda a yau ya zama Talaka bai ma san kan sa ba. Babban abin tashin hankalin ma shine su wadannan 'yan siyasar na yau a cikinsu akwai 'ya'ya da ma jikokin NEPU. Kuma har zuwa yau suna iya tutiya ko da'awar cewa su ma 'yan NEPU ne ko kuma akwai jinin NEPU a jikinsu. To amma fa duk karya ce ihun kawai!